# MUJALLAR CITAD RADIO
## RADIYON DA ZAKU SAURARA
## www.citad.org/radio

Volume 1, issue 7

-10-1442 AH
26-06-2021 AD


*CIBIYAR BUNKASA FASAHAR SADARWA DA CIGABAN AL'UMMA (CITAD) NA BAYAR DA HORO KAN ILIMIN NA'URA MAI KWAKWALWA*

## LABARAN CIKI


| | |
|---|---|
| **Muryar Matasa** | 1 |
| **Watch Dog** | 2 |
| **Ilimin 'Ya Mace** | 3 |
| Sharhin Yau da Kullum | 4 |
| **Shiri Na Mussamman** | 5 |
| **Siyasa Da Rayuwa** | 6 |
| **Ilimi Da Matasa** | 7 |


**Zaku iya sauraro da sauke manhajar CITAD RADIO ta wannan likau din dake kasa**



*https://play.google.com/store/apps/details?id=com.citad.org&hl=en&gl=US*

# CITAD Ta Gabatar Da Sababbin Littattafan Da Ta Wallafa A Jami'ar Maiduguri

A cigaba da gabatar da littattafan da Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwar da Cigaban Al'umma, CITAD, ta wallafa waɗanda su ka mayar da hankali akan yadda cin hanci da rashawa su ka dabaibaye ɓangaren tsaron ƙasar nan da kuma yadda kalaman ƙiyayya kan haifar da tarzoma tare da ƙara rura wutar rikici a tsakankanin al'umma.

A Litinin da ta gabata ce wakiliyar cibiyar ta CITAD, Malama Hassana I Waziri, Malama a sashen kimiyyar siyasa na jami'ar Maiduguri, ta gabatar da littattafan guda biyu a harabar jami'ar ta Maiduguri.

Littafi na farko mai suna The Compromised State:

How Corruption Sustained Insecurity in Nigeria, wanda ya mayar da hankali akan yadda cin hanci da rashawa ya dabaibaye ɓangaren tsaron ƙasar nan aka kasa samo bakin zaren.

Sai kuma littafi na biyu

## Cibiyar CITAD Za Ta Yi Bikin Ranar Masu ƙananan Masana'antu Ta Duniya

A ƙoƙarinta na lalubo hanyoyin da za su bunƙasa kasuwancin masu ƙananan masana'antu tare karfafa musu gwiwa, Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Cigaban Al'umma, CITAD za ta yi bikin ranar masu ƙananan masana'antu ta duniya a ranar 27 ga watan Yunin Shekarar 2021. A ranar bikin fitacciyar yar kasuwar nan a shafukan sadarwa na zamani, kuma shugabar kamfanin Gatmeals za ta gabatar da ƙasida mai taken 'Kalubalen Da Ƙananan Yan Kasuwa Ke Fuskanta A Yankin Arewacin Najeriya' Inda masanin tattalin arzikin nan na Kwalejin Ilimi ta Sa'adatu Rimi da ke Kano, Dakta Abdussalam Kani zai kasance mai yin sharhi tare da sanya ido. Masu ƙananan masana'antu a yankin Arewacin Najeriya dai sun dade suna kokawa game da rashin hanyar fitar da kayayyakinsu zuwa kasuwannin duniya, abinda suka ce yana kawo musu nakasu wajen bunkasar tattalin arzikinsu. su.

## Jabun Maganin Gargajiya Ya Yi Sanadiyar Rasa Rayuka 10 a Najeriya




A jihar Kwara dake kasar Najeriya, mutane 10 sun mutu bayan sun sha jabun maganin gargajiya. Kakakin rundunar ‘yan sanda na jihar Kwara Ajayi Okasanmi ya sanar da cewa, mutane 10 ‘yan gida daya sun rasa rayukansu bayan sun sha maganin gargajiya na bogi, wanda ake ikirarin na sarkar da ciwon kafa a garin Gwanara.

Da yake lura da cewa an tura jami’an kiwon lafiya zuwa yankin, Okasanmi ya ce an fara bincike game da lamarin.

Okasanmi ya bukaci jama'a da su nisanci irin wadannan shaye-shayen magunguna.



## CITAD Tai Zagayen Makarantu, dan Nuna musu Amfanin Fasahar sadarwa da Nuna Sha'awa kan Na'ura mai Kwakwalwa.

A kokarin ganin daliban da suke shirin gama manyan makarantun sikandire sun sam dammar damwa da su a harkar fasahar sadarwa, cibiyar bunkasa fasahar sadarwa ta ziyarci wasu makarantu a cikin kwaryar birinin kano dan gabatar musu da mukala kan wannan batu. Daga cikin makarantun da CITAD din ta ziyarta sun hada da GGSS Yakasai, Jami’an dai Cibiyar ne dai suka gabatar da takardu da kuma bayanai ga daliban a lokacin gabatar da mukala, zagayen dai ana gudanar da shi ne duk shekarar dan ganin alfanun fasahar sadarwa na na’ura mai kwakwalwa dan cigaban al’umma.

CITAD

**CENTRE FOR INFORMATION TECHNOLOGY AND DEVELOPMENT (CITAD)**

3rd Floor, NSITF Building, No. 1A, Social Insurance Road,
Behind Trade Fair Complex ,Off. Zaria Road, Kano
E-mail: info@citad.org Website: www.citad.org

**WE OFFER THE FOLLOWING COURSES**

**Certificate in Information Technology (CIT) 8 Weeks**
**Certificate in Digital Marketing (CDM) 1 Week**
**Certificate in CIT for Families 1 Week**
**Certificate in Digital Entrepreneurship (Freelance) 1 Week**
**Diploma in Information Technology (DIT) 8 Weeks**
**Diploma in Graphics Design (DGD) 8 Weeks**
**Diploma in Data Analysis (DDA) 6 Weeks**
**Diploma in Computer Repairs and Maintenance (DCRM) 8 Weeks**
**Diploma in Mobile App Development without Codin (DMAD) 8 Weeks**
**Diploma in Mobile App Development with Codin (DMADC) 12 Weeks**
**Diploma in Auto Card (DAC) 8 Weeks**
**Diploma in Website Design (DWD) 8 Weeks**

**Our Executive Classes**
**Certificate in Information Technology (CIT) & Diploma in Information Technology (DIT)**

**OUR VISION is:**
A knowledge-based democratic and self-reliant society

**OUR MISSION is:**
To empower citizens for a just and knowledge-based society that is anchored on sustainable and balanced development using ICT, Capacity Development, Advocacy, Research and Partnership

**OUR CORE VALUES are built on the following principles:**
Responsibility:
Responsiveness:
Reliability:
Integrity:
Transparency:
Accountability:

For enquiry:
08063998787
E-mail: info@citad.org
Website: www.citad.org

CITAD

**Celebration of International Day of Micro, Small and Medium Enterprises**

*Topic:*
*Challenges Young Entrepreneurs Are Facing in Northern Nigeria and Experience Sharing *

**Discussant**

Maryam Gatawa, Chief Executive Officer, Gatmeals

**Moderator**

Dr. Abdussalam Muhammad, Kani, Lecturer Dep. of Economics, SRCOE

**Venue: Hall B, CITAD, Kano**

**Time: 4pm**

**Date: Sunday, 27 June, 2021**

WWW.CITAD.ORG/
RADIO

Main Office:3rd Floor, NSITF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 080-68078282
080-54362931
070-33427467
E-mail: info@citad.org,
Website: www.citad.org

www.citad.org

**Center For Information Technology and Development**

**BABBAN EDITA**
Hamza Ibrahim

**EDITA**
Buhari Abba Rano

**MATAIMAKIN EDITA:**
Gazzzali Haruna

**MAI KULA DA TSARE-TSAREi:**
Ali Sabo

**Mai Kula Da Dab'i**
Salim Sani Shehu

**Manyan Masu Garkuwa Da Mutane Mafiya Haɗari Da Ke Laɓe A Cikin Gwamnati.**

***Y.z Yau***

Duk da kasancewar muna cike da tsoron mutanen da su ke yin garkuwa da mu domin karɓar kuɗin fansa, to amma akwai wani rukunin waɗansu mutane da su ke da matuƙar hatsari fiye da masu garkuwar dan karɓar kuɗin fansa.

Waɗannan jinsin mutane da ba su fito ƙarara sun yi garkuwa da mu ba, amma tuni sun yi garkuwa da ɗaukacin al'ummar Najeriya tare kuma da karɓar maƙudan kuɗaɗen fansa ba tare da an tattauna ba.

Su waye wadannan jinsin mutanen? Ba wasu ba ne face mutanen da aka damka musu amanar riƙe shugabancin ƙasar nan domin su samarwa da al'umma ingantaccen tsarin ilimi mai nagarta da samar musu da tsarin kiwon lafiya mai aminci da kyau tare kuma da samar da ingantaccen tsaro.

Haka kuma su ne za su samar da wani yanayi da zai samarwa da ɣan ƙasa ayyukan yi da sauran abubuwan more rayuwa.

Sai dai a maimakon su yi waɗannan ayyukan da za su inganta rayuwar al'ummar ƙasa, sun ɓige da satar dukiyar ɣan ƙasa wanda hakan ya jefa al'umma cikin matsananciin talaucin da ya hanasu samun ingantaccen kiwon lafiya, hana ɣaɣan talakwa samun nagartaccen ilimi tare kuma da haifar da rashin ayyukan yi. Kuma rashin aikin yi ga ɗimbin matasan ƙasar nan ne ya haifar da matsalar tsaron da ta kai ga ana yin garkuwa da al'umma domin su samu abin da bai kai ya kawo ba domin biyan buƙatar kan su.

Sun yi wasti da matakan da ake bi wajen tafiyar da kyakkyawar gwamnati ga al'umma a maimakon hakan sun mayar da kan su gungun miyagun mutane kuma matsafa da su ke jan ragamar shugabancin al'umma.

A kullum harkar tsaro a ƙasar nan ƙara ta'azarra ta ke yi wanda hakan yana faruwa ne sanadiyyar gazawar gwamnati wajen yin amfani da dukiyar ƙasa domin yin abin da ya kamata musamman samawa ɗimbin matasa ayyukan yi ta hanyar farfaɗo da tattalin arzikin Najeriya.

Dalilin ayyukan waɗannan ɓoyayyun masu garkuwa da mutanen ne ya haifar da masu garkuwa da mutane da mu ke ganinsu a zahiri, wanda hakan ne ya sanya mu ka tsinci kan mu a salon nan na masu iya magana da kan ce "Ga Mari Ga Tsinka Jaka", wato masifa biyu ke nan!

A kullum ya kamata mu dinga tunawa cewa a duk lokacin da aka yi kuwwar an kama masu garkuwa da mutane to mu sani cewa akwai ɗaruruwan su da su ke cikin ofis su ke cigaba da garkuwa da Ni da Kai da kuma Yaɣan mu ta hanyar wawure dukiyar al'umma.

Hakazalika a kullum suna cigaba da yin garkuwa da mu ba tare da sun yi amfani da ko bindigar wasan yara ba, sai dai sakamakon mugun aikin na su shi ne ya haifar da masu garkuwar da ke dauke da muggan makamai a dazukan Kamaku da Rugu da kuma sauran guraren da su ka yi sansani.

Mu sani cewa waɗannan miyagun shuwagabannin suna nan hankalinsu kwance a gidajen gwamnati da kuma manya - manyan ofisoshin jami'an gwamnati da ke faɗin ƙasar nan. Haka kuma dangantakar miyagun ayyukansu da masu garkuwa da mutane da su ke dazuka shi ne ya ke mayar da hannun agogo baya tare da wahalar da ɗimbin al'ummar ƙasar nan wajen zama lafiya da kwanciyar hankali.